# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na goma sha biyar: Kyan tafiya dawowa

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Magaji: | ɗan shekara 22 |
| Jami’in shige da fice: | ɗan shekara 40 |
| Lami: | ’yar shekara 20 |
| Sa’adatu: | ’yar shekara 35 |
| Charles: | ɗan shekara 45 |
| Ɗan sanda: | ɗan shekara 35 |
| Faisal: | ɗan shekara 19 |
| Roda: | ’yar shekara 25 |

**Mai gabatarwa:**

Jama'a, muna yi muku marhabun lale a ciki wannan shirin namu na "Ji ka Karu". Wannan shi ne kashi na goma sha biyar kuma na ƙarshe a cikin jerin wasan kwaikwaiyon da muke kawo muku ta wannan gidan rediyon mai taken "Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai". A wancan kashin da ya gabata, Lami ta yi wa babarta waya cikin tsakar dare, kira irin na neman ɗauki, tana neman gafara, amma ta ƙi faɗa wa babar tata abin da ya faru.

Ku biyo mu don ku ji abin da zai faru a wannan kashin na yau mai suna "Kyan Tafiya Dawowa". Za mu fara wasan namu ne daga inda Magaji ya sauka a tashar jirgi kusa da jami'a inda yake tambayar jami'i mai ba da bayanai, yana tambaya.

**Fitowa ta 1 : Magaji ya iso tashar jirgi a cikin gari**

**Magaji:** Barka da warhaka. Don Allah ta ina zan bi in je jami'a? Ina neman tsangayar koyon ilimin shari'a ne.

**Mai ba da bayanai:** Malam saurara, nan fa wajen neman bayanai ne a kan tashar jirgin ƙasa, ba ofishin 'yan yawon buɗe ido ba ne. Ba abin da zan iya faɗa maka sai bayanin lokutan zuwan jirgin da tafiyar jirgin ƙasa. Idan kana neman hanyar zuwa wani wuri ne ko taswirar cikin gari, to ina ba ka shawara da ka je wurin ba da bayanai na 'yan yawon buɗe ido.

**Magaji:** Ka ga, na sha wahala a ɗan tsakanin nan matuƙa. In dai ka san hanyar zuwa jami'ar, me zai hana ka faɗa min? Na yi maka kama da ɗan yawon buɗe ido ne? Ba abin da ya kawo ni nan ke nan ba. Don haka kada ka ce min in je ofishin 'yan yawon buɗe ido.

**Mai ba da bayanai:** Ok, ok, ya isa! Jami'ar ba ta da nisa daga nan. In ka fita

daga nan, bi hagu, ka yi ta tafiya har ƙarshen hanya, sai ka koma dama, za ka hau kan babbar hanya, sai ka yi tafiyar kimanin minti biyar. Za ka ga jami'ar a gabanka.

**Magaji:** Na gode. Sai an jima.

**Mai ba da bayanai:** To shi ke nan, sai an jima.

**Mai ba da labari:**
Zuciyar Magaji sai bugawa take ta yi yayin da ya kama hanya, ga shi gab da masoyiyarsa, Lami Talle. Wani mai gadi a ƙofar shiga jami'ar ya kwatanta masa inda ɗakinta yake. Yana hawa mattakalar bene cikin sauri, yana tuna lokacin da suka taso shi da ita tun suna ƙanana. Nan da nan sai ga shi a ƙofar ɗaki mai lamba 316. Akwai wata 'yar guntuwar takarda da aka rubuta 'Lami Talle' a liƙe jikin ƙofar.

**Lami:** Wane ne? … Tsaya, ina zuwa.

**Magaji:** Sannunki, masoyiyata ta kaina.

**Lami:** Lalala! Magaji?! Anya kuwa kai ne? Kai ne ka zo?

**Magaji:** Ai na faɗa miki ba abin da ba zan yi ba saboda ke, to ga shi na tsallako teku saboda ke Lami, kamar yadda na faɗa.

**Lami:** Kai… Kai ka zo! Kai kuwa ta yaya ka shigo? Shigo mana Magaji, shigo ciki! Shigo ka sha labari!

**Magaji:** Haka ne? Ni ma ina da labarin da zan ba ki.

**Mai ba da labari:**
Magaji da Lami sun ɗauki dogon lokaci suna ba juna labarin irin halin da suka shiga, da gwagwarmayar da suka sha a Turai. Daga ƙarshe dai Lami ta bayyana masa batun auren bizarta da Charles don ta sami takardar izinin yin aiki. Ta ma ji daɗi tun da yanzu ta huta da wannan jidalin. Yau da safen nan ta sami wasiƙar cewa, hukuma ta warware wannan auren.

**Lami:** Don Allah ka yi haƙuri Magaji. Na sa ka a wahala mai yawa a yayin da nake auren wani, kuma abin takaicin ma shi ne, na kasa faɗa maka gaskiya. A gaskiya ban cancanci soyayyarka ba. A tawa wautar ina ganin abin da na yi shi ne daidai. Amma fa ba wani abu da ya taɓa gudana tsakanina da Charles. Duk da haka ina ganin na ci amanarka. Don Allah ka yafe mini! Amma ai yanzu ma iya sake buɗe sabon shafi ko? Wasiƙar da aka kawo daga kotu ta nuna cewa a yanzu ba ni da aure.

**Magaji:** To, amma ke kuwa me ya kai ki yin wannan, Lami? Kin yi alƙawari za ki aure ni. Me ya sa kika auri wani a nan?

**Lami:** Ba yadda zan yi ne, abin ya zame min dole. Ina matuƙar buƙatar kuɗi. Haba Magaji, ina haɗa ka da Allah ka yi haƙuri! Ka yafe ni!

**Magaji:** Zan miƙa kaina ga hukuma, Lami. Ban san yaya za su yi da ni ba. Amma ina fatan kada su kai ni kurkuku, ina fatan su mai da ni gida kawai. Na haɗu da wani da ya ba ni shawarar cewa duk abin da zan yi, na yi shi bisa ƙa'ida. Ina ga lokacin jarraba hakan ya yi.

**Lami:** Magaji, har yanzu kana so ka aure ni?

**Magaji:** Lami, kada ki yi min wannan tambayar yanzu. Hankalina ba ya jikina. Ban san me ya kamace ni ba ma. Na san dai dole na koma gida. Kina iya biyo ni idan kina so.

**Mai ba da labari:**
Bayan 'yan kwanaki Magaji ya miƙa kansa ga hukuma, kuma nan take suka mayar da shi inda ya fito. A ɗaya ɓangaren kuma, an mai da Faisal sansanin 'yan gudun hijira inda rayuwar da ya yi ta mafarkin samun ta tsawon lokaci ta fara bayyana, wato rayuwar ɗan gudun hijira a Turai

**Fitowa ta 2: Faisal a sansanin 'yan gudun hijira**

**Faisal:** Ni ba haka na ɗauki abin ba. Ba wani 'yanci a nan. Na ɗauka komai zai warware da zarar na shigo Turai, amma da alama akwai sauran aiki a gaba. Ba ni da kowa a nan, ga ni nan ne dai kawai. Amma kuma ba zan iya komawa gida ba saboda ai sai a yi min dariya. Amma ina jin nan ɗin dai zai yi. Da zarar na cancanci mallakar muhalli nawa na kaina, ta yiwu abubuwa su daidaita. Sai dai kuma ban san yaushe ne hakan za ta faru ba. Ga shi har yanzu ba ni da kuɗi, kuma za a iya ɗaukar shekaru kafin a ba ni damar fara aiki. Kai!...

**Mai ba da labari:**
A can kuma Afirka, Magaji ya koma kan aikinsa na da, kuma ya ci gaba da harkokin rayuwarsa na yau da kullum. A halin yanzu ma yana gidan su Lami, ya je duba babanta wanda yanzu ya warke sarai daga raunin da ya samu, yana kuma faɗa masa abin da mutane suke ta cewa.

**Fitowa ta 3: Magaji a gidan su Lami da yamma**

**Magaji:** Wallahi da gaske nake! Mutane sun ɗauke ni wawa, wai don na zaɓi zaman Afirka a kan na Turai.

**Matar M. Talle:** E to, ni fa ba na ganin laifinsu.

**Malam Talle:** Wato abin da yake ɗaure min kai shi ne, bayan duk wahalar da ka sha har ka samo Lami, amma ba ka aure ta ba kuma. Na ɗauka abin da ya kai ka ke nan, ko ba haka ba ne?

**Matar M. Talle:** To, alhamdu lillahi dai tun da ga shi abubuwanka na tafiya yadda ya kamata. Allah ma dai Ya sa ka nemi hutu kafin ka tafi, da yanzu sai ka sha wahala kafin ka sami wani aikin.

**Magaji:** Gaskiya ne. Amma na tabbatar akwai damammaki a nan Afirka waɗanda har yanzu ba ma amfani da su sosai. Ina mamaki, ko me ya sa mutanenmu suke son tafiya wani wuri inda da ma komai ya zauna da gindinsa, maimakon mu kafa su a nan Afirka!

**Malam Talle:** Mu da ma tunaninmu ke nan, amma daga baya mun gano cewa mafarki ne kawai. Ba shakka akwai damammaki a Afirka, amma ba kowa ake ba wa su ba, sai shafaffu da mai. Ga Lami alal misali, yanzu ba don ta je Turai ba wa zai biya min kuɗin asibiti?

**Magaji:** Amma Baba, ban tari numfashinka ba, ni a tunanina ba haka ba ne. Ni har yanzu ina ganin zai fi dacewa a ce Lami ta ƙarasa karatunta a nan. Za ta iya samun aiki mai ƙwari a wani babban ofishin lauyoyi. Ta ma iya buɗe ofishinta don ta ci gashin kanta.

**Matar M. Talle:** Ofishin lauyoyi masu ma'amala ta ƙasa da ƙasa a nan? To a ina za ta sami kwastomomi?

**Magaji:** Haba, wannan ba matsala ba ce. Ki yi la'akari da tuhumar da Kotun Duniya ta birnin Hague take yi wa 'yan siyasa da shugabannin Afirka mana. Wannan kotun tana da ofisoshi masu yawa a Afirka. Wallahi irin waɗannan lauyoyin suna samun kuɗi ba kaɗan ba.

**Malam Talle:** Haka ne. Sai dai kana da tabbacin hakan kuwa, Magaji? Amma duk da haka na ji daɗi ta je waje duk da cewa karatun nata ya lashe dukan abin da muka mallaka.

**Matar M. Talle:** Muna sa ran zuwan wani baƙo ne?

**Malam Talle:** Anya kuwa? Ban san da zuwan wani baƙo ba. Amma kuma ai dare ya ɗan yi yanzu. Magaji, ko za ka leƙa ka ga ko wane ne?

**Magaji:** Me zai hana.

**Lami:** Au masoyina kai ne?

**Magaji:** Lalala, Lami! Ke ce? Me ya dawo da ke?

**Lami:** Na dawo gida ne mana! Ko ba ka barka da zuwana ne?

**Magaji:** A'a, yaya za ki ce ban a barka da zuwa? Sannu da zuwa!

**Matar M. Talle:** Lami! Ke ce?

**Malam Talle:** Lami, me ya dawo da ke kuwa?

**Lami:** Sannunku, Baba da Mama! Na dawo gida ne, ko ba kwa maraba da ni?

**Malam Talle:** A'a, muna maraba!

**Magaji:** Kina nufin kin dawo ke nan gaba ɗaya? To karatun naki fa?

**Lami:** Ina so na ƙarasa shi a nan gida, cikin mutanen da nake ƙauna suke ƙaunata. Baba, yaya jikin naka?

**Malam Talle:** Jiki da sauki. Wai me kike cewa ne, Lami? Me kike nufi da za ki ƙarasa karatunki a nan? Saura shekara ɗaya da rabi fa ki gama!

**Lami:** Baba, ka yi haƙuri don kuwa na ba ka kunya. Amma na riga na yanke shawara. A nan ƙasa zan ƙarasa karatuna.

**Matar M. Talle:** Shawarar da Magaji ya ba ki ke nan da ya je wajenki? Ki yi watsi da rayuwarki ta Turai ki dawo nan, wannan nahiyar da aka wanke mata hannu a ka? To saboda me? Saboda ya aure ki, rayuwarki ta ƙare a kicin?

**Magaji:** Mama, me kike faɗa haka?

**Lami:** Don Allah Mama, daina faɗar wannan magana!

**Malam Talle:** To ya isa haka, kowa ya kwantar da hankalinsa.

**Magaji:** Gara ma na tafi. Kina buƙatar ki ɗan huta. Ina yi miki barka da zuwa, Lami.

**Lami:** Na gode Magaji, amma don Allah… ɗan dakata ka rufe ƙofar nan in ba za ka damu ba. Abin da zan faɗa wa Baba

da Mama ya shafe ka kai ma. Lokaci ya yi da zan yi abin da ya dace…

**Mai gabatarwa:**

Magaji dai ya rufe ƙofa don ya saurari abin da Lami za ta faɗa. Kuma da wannan ne muka kawo ƙarshen wannan kashi na goma sha biyar kuma na ƙarshe daga jerin wasan kwaikwayonmu da muke kawo muku ta wannan gidan rediyo mai taken “Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai”, wanda Chrispin Mwakideu za rubuta.

Mene ne ra’ayinku game da yin ƙaura ko gudun hijira zuwa Turai da kuma sauran abubuwan da muka ji a wannan wasan? Ku ziyarci dandalin tattaunawarmu a facebook.com/dw.lbe. Haka kuma kamar kullum, idan kuna son sake sauraron wannan kashin, ko kuma wani kashin da za gabata, kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato de.de/lbe. A halin yanzu ku huta lafiya.

**’Yan wasa:**

Shehu Ali Shagari
Buhari Ibrahim
Maryam Mohammed Ibrahim
Habiba Inuwa
Zainab Bala
Munir Isa
Ɗan Fulani
Yunusa Musa
Yusuf Idris
Huraira Ibrahim
Bulus John
Ruƙayya Bala
Neeta Yusif
Kabiru Mohammed
Zainab Ibrahim
Ado Muhammed
Lola Abdulkadir